**EPISODE 14**

**<u>Characters</u>**

*Asabe*

*Laraba*

*Inna*

*Husseini*

*Alhaji Bature*

*Safiya*

**Scene 1**

**Hajiya Inna's residence.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |
| 2. | **SFX:** | **<u>SOUNDS OF DOORS CLOSING AND FOOTSTEPS</u>** |
| 3. | **LARABA:** | Ah Asabe, Salam alaikum. |
| 4. | **ASABE:** | **(MOCKING)** Laraba kenan, mai iya kama maza! |
| 5. | **LARABA:** | **(TAKEN ABACK)** Ah Asabe, b*an gane ba* |
| 6. | **ASABE:** | *Zaki gane,* Laraba, *Zaki gane, kina ji na?* |
| 7. | **LARABA:** | *Sai kin ganar da ni dai* |
| 8. | **ASABE:** | Laraba, mai yasa kullun kina tare da maza dabban dabban a kofar gidan nan? |
| 9. | **LARABA:** | Haba Asabe, ba haka, bane fa, ni ban taba gayatar wani ba kuma ina fada musu kada su sake zuwa |

| | | |
|---|---|---|
| 10. | **ASABE:** | (**CLAPS HANDS TOGETHER LOUDLY**) Haka ki kache Laraba! Amma kina amfani da kayan mata ai na kiran maza |
| 11. | **LARABA:** | **(SHOCKED)** Asabe, wane irin kayan mata na kiran maza kuma? |
| 12. | **ASABE:** | **(SUCKS TEETH )** Kina tsamanin ni bakauyiya ce, harma ban san mata kamar ki na amfani da kayan mata kiran maza ba? |
| 13. | **LARABA:** | **(INTERRUPTS)** *Ni?! Kayan mata?!* |
| 14. | **ASABE:** | E mana! Na san kice babbar kastoma na matan nan da ke sayarwa a babbar kasuwa |
| 15. | **LARABA:** | *Haba* ASABE.baki da hankali ne, wace irin zance ne wannan |
| 16. | **ASABE:** | Ahhhh! Laraba *Wato rashin hankaline neman sanin menene dalilin da kika maida min iyaya masu jira a kofa? Kullun suna fama da isar da sakon maza daban daban,* |
| 17. | **LARABA:** | **(EXCLAIMS)** Hmm, Asabe, *lafiyan ki kuwa*? |
| 18. | **ASABE:** | (**SUCKS TEETH LOUDLY**) Laraba, don na baki gida kuma nayi miki shiru ko…... |
| 19. | **LARABA:** | **(INTERRUPTS)** Asabe kin san dai ina mutuntakiki, ya kuma kamata kema ki bani girma ta, |
| 20. | **ASABE:** | Laraba, ki gaya min,ina dalilin da azan mutunta wace bata san mutuncin kanta ba?! Ai ke abin kun ce wa mata |
| 21. | **LARABA:** | **(INSULTED)** Asabe, don wannan zagen saboda menene? Allah ya isan min har abada, Allah zai saka min |
| 22. | **ASABE:** | **(RUDELY)** *Ya isa mana tare,* Laraba |
| 23. | **LARABA:** | Hakika Asabe kina hauka |

24. **ASABE:** Ai gwanda hauka da yin abin kunya na neman maza dabban dabban, Laraba, kin dai san abin da ake cema irin halin ai ko?

25. **LARABA:** **(GASPS LOUDLY)** Ne?! Asabe, abin naki yayi yawa!

26. **ASABE:** Hmmm! Amaimakon ki zabe daya da cikin mazajen da kike bi ki aura, kina nan kina jin kanki tamkar sarauniya.

27. **LARABA:** Asabe, kiyi min shiru! Kina ji na ko?!

28. **ASABE:** **(YELLING)** Laraba, amma idan baza ki natsu saboda nib a me yasa baza ki natsu saboda yata Raliya ba? Kina son ki bata ta ne?

29. **LARABA:** **(ANGRY)** Ki saurara Asabe, ne dai saurayi guda nake dashi, shine Dr. Daoud, kuma ai Raliya yar shekaru biyu me ta sani?

30. **ASABE:** Baturiya! Ki maida ne wawuya domin ban yi boko kamar naki ba!

31. **LARABA:** **(IRRITATED)** Asabe, kin fiye juya zace…. Ne dai ki kyali ne, kiyi abinda ta shafe ki

**32.** **SFX:** **(<u>SOUND OF DOOR BANGING</u>)**

33. **ASABE:** **(SHOUTING)** Ta shafe ne, Laraba! Kina ji na, ta shafe ne! saboda nan gidan mijina ne, idan baki son in yi Magana akai kiyi aure

34. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 2**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's room**

35. **SFX:** (**<u>SOUND OF QUICK FOOTSTEPS</u>**)

36. **INNA:** **(CALLING OUT)** Laraba! Laraba!!

37. **LARABA:** Na'am Inna

| | | |
|---|---|---|
| 38. | **INNA:** | Haba Laraba, ina zaki kike sauri haka? Kice kika buga kofar haka? |
| 39. | **LARABA:** | **(AGITATED)** Kiyi hakuri Hajiya, ina son in fita saboda bakin Asabe |
| 40. | **INNA:** | Shigo cikin daki na, ina son inyi miki wata Magana |
| 41. | **SFX**: | **<u>(SOUND OF DOOR CLOSING FOLLOWED BY FOOTSTEPS, THEN SOUND OF BED CREAKING AS BOTH WOMEN SIT ON IT)</u>** |
| 42. | **INNA:** | Bana fada miki ki daina biye ma Asabe ba, Laraba! |
| 43. | **LARABA:** | **(DEFENSIVELY BUT RESPECTFUL)** Inna, itace ki shishige min harkokina |
| 44. | **INNA:** | Me ya faru kuma yanzu? |
| 45. | **LARABA:** | Hajiya, wani yazo wuri na da na shigo ciki, sai ta kama gaya min maganganu daban daban |
| 46. | **INNA:** | Wani? |
| 47. | **LARABA:** | tun da nazo garin nan, maza da dama suka nuna min suna sona amma cikin hikima naki ki |
| 48. | **INNA:** | Me yasa kike kin su? Me yasa baza ki zabi guda ki aura ba? |
| 49. | **LARABA:** | **(LAUGHS SHYLY**) Na zabi guda ai, kuma shine ya zo gani na |
| 50. | **INNA:** | Haba? |
| 51. | **LARABA:** | sunan sa Dr. Daoud |
| 52. | **INNA:** | Ah! Likita!nayi miki murna kwarai |
| 53. | **LARABA:** | **(HAPPY)** Nagode Inna |
| 54. | **INNA:** | Ai, ki za’a ma godiya! Kin taimaka wa iyalai dayawa ta hayan aikin nuna muhimuncin tazaran haihuwa |

| | | |
|---|---|---|
| 55. | **LARABA:** | Hajiya, ni ina jin dadin aikin taimaka wa jama'a. |
| 56. | **INNA:** | Abinda ke mutukar faranta min rai, shine har yayana da matansu kin iya kin taimaka masu |
| 57. | **LARABA:** | nima nayi farin ciki iya taimaka masu wurin tabbatar da sun same iyalin da suke so kuma suna iya lura dasu cikin kwancin hankali |
| 58. | **INNA:** | ai hakika lokacin mu na da, abu mai wuya ne ma aurata su aminci da hayoyin tazaran haihuwa |
| 59. | **LARABA:** | **(INTERESTED)** haba? Tor yaya kuke yi a da? |
| 60. | **INNA:** | Abinda muke yi ada, muna zama da iyayen mu sama da kwana 40 din da aka sani, wasu lokuta ma har wattani |
| 61. | **LARABA:** | Amma ma aurata sun sha wuya da |
| 62. | **INNA:** | Hakika wuya sosai fa, mamata |
| 63. | **LARABA:** | Ai, hanyoyin tazaran haihuwa na zamani na bada damar ma aurata su zauna tare, a natsi kuma yana biyan bukata |
| 64. | **INNA:** | Zamani ai sai hamdalla |
| **65.** | **LARABA:** | Gaskiyan ki Hajiya Inna, mudan ma aurata sun bi kaidodin da aka kaidanci wa hanyar tazaran haihuwa da suka zaba, tor suna da kwancin hankali |
| **66.** | **MUSIC:** | **BRIDGE MUSIC** |

**Scene 3**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's House. Outside. Morning.**

| | | |
|---|---|---|
| 67. | **HUSSEINI:** | Salam alaikum, Asabe. |
| 68. | **ASABE:** | Walaikum salam, Husseini. Mai gida, an dawo? Yaya aikin yau? |
| 69. | **HUSSEINI:** | Matata, na dawo fa. Aiki lafiya, yaya gidan? |

| | | |
|---|---|---|
| 70. | **ASABE:** | **(SUCKS TEETH)** Hhhmm Husseini, baka san abinda shashashar matan nan tayi min a cikin gida na ba. |
| 71. | **HUSSEINI:** | Wacece? |
| 72. | **ASABE:** | Wacece kuwa idan ba Laraba ba? |
| 73. | **HUSSEINI:** | Asabe, me tayi miki? |
| 74. | **ASABE:** | Hmm mai gida, tayi min rashin kunya da reni sosai yau |
| 75. | **HUSSEINI:** | Toh, |
| 76. | **ASABE:** | bata da kunya, kuma duk abinda ta keyi tana son a dinga ganinta |
| 77. | **HUSSEINI:** | Mhm |
| 78. | **ASABE:** | **(UPSET)** Maigida, baka ma sauraron abinda nake fada maka kuma |
| 79. | **HUSSEINI:** | Ina sauraron ki mana |
| 80. | **ASABE:** | **(ANGRILY)** Baka saurarao! |
| 81. | **HUSSEINI:** | Tor? **ASABE:** **(CONCERNED)** Ha! Maigidana kamar ba kai ba, me ke damun mijina ne? |
| 82. | **HUSSEINI:** | Na shawarce Hassan yayi takarar kamsilar mazabar nan |
| 83. | **ASABE:** | **(IMPATIENT)** E na sani, Jummai ma ta gaya min ciwa fustocin takarar zasu fito mako nagaba, kaga anan za'a gani cewa muna da muhinmanci anan al'umar, kuma duk aikin kane ai |
| 84. | **HUSSEINI:** | **(INTERRUPTS)** Asabe akwai matsala fa, mai gidana Alhaji Bature yana da dan takkararra da yake so, yanzu yana son in yi ma Hassan Magana ya jinye takarar sa |
| 85. | **ASABE:** | Kai! Husseini! |

| | | |
|---|---|---|
| 86. | **HUSSEINI:** | Gaskiya! Alhaji Bature yadage sai na sha kan Hassan ya yanye takarar sa |
| 87. | **ASABE:** | **(SUCKS TEETH)** Ahhh wane irin matsala ce wannan kuma? Tor tashi ka tafi gidan Hassan ka sanar da shi, inna ganin zai janye takarar indan kuka yi magana |
| 88. | **HUSSEINI:** | **(INTERRUPTS)** Kai! Asabe, aina je |
| 89. | **ASABE:** | Toh, meyasa ka hada rai? |
| 90. | **HUSSEINI:** | Kin san Hassan da yadda yake yin abubuwa kamar bature; yace bazai janye takarar ba wai saida a yi zabe wanda ke da jama'a ya ci |
| 91. | **ASABE:** | **(ANGRILY)** Kai Husseini meyasa danuwan ka baya la'akari da abubuwa ne wasu lokutan? Duk da cewan ya riga da ya buga fustocin takarara , ai yak mat yay i hakuri saboda kai ma. |
| 92. | **HUSSEINI:** | Ai ya ma ce ko da bai kasha kudin buga fustocin takararar ba, bazai janye ba saboda ra'ayi irin tasa |
| **93.** | **ASABE:** | **(UPSET)** tor abin da y ace kenan, Husseini! Lallai sai an fada ma Inna, na tabbabta zata iya sa shi ya janye |
| **94.** | **MUSIC:** | **BRIDGE MUSIC** |

**Scene 4**

**Alhaji Bature's residence. Late Evening**

| | | |
|---|---|---|
| 95. | **SFX:** | **SOUND OF CROCKERY AND CLINKING OF CUTLERY** |
| 96. | **ALHAJI:** | **(PLEASED)** Laila sabuwar amarya ta, uwar girki Safiya! |

| | | |
|---|---|---|
| 97. | **SAFIYA:** | **(GIGGLES)** Ah, Alhaji Bature, ka daina! duk wannan yabon saboda dan abincin da na girka? |
| 98. | **ALHAJI:** | Bazan iya daina w aba ai! Girkin ki da dade kwarai, kinga har lasan yatsu nakeyi |
| 99. | **SAFIYA:** | **(LAUGHS)** Ah mai gida, inna rawa |
| 100. | **ALHAJI:** | ai kin iya girki kwarai, masoyiyata |
| 101. | **SAFIYA:** | yayi fa! Nayi murna ka ji dadin abincin |
| 102. | **ALHAJI:** | **(CLAPS)** Yauwa, yanzu na dawo mutun amma dazu yinwa nake ji ainun |
| 103. | **SFX:** | **<u>(SOUNDS OF CROCKERY AS PLATES ARE STACKED</u>)** |
| 104. | **SAFIYA:** | mai gida bara in kwashi wadannan kwanukan inma wanke su |
| 105. | **ALHAJI:** | **(INTERRUPTS)** safiya, idan kin haifi yara ba sai kin dinga yin yan aikeaike nan ba, zasu tallafa miki, sai yasa ya dace kin yi hanzarin daukar ciki, ko? |
| 106. | **SAFIYA:** | **(UPSET)** Alhaji Bature duk lokacin da muke tare sai zacen daukar ciki da yara kake yi, don Allah mu bar zacen mana! |
| 107. | **ALHAJI:** | Safiya, an yi kwana biyu da dauren auren mu, bai yakamata ya sha min kai bane? |
| 108. | **SAFIYA:** | **(ANGRILY)** Haba? Sai yasa kake yawar matsa min, bana ma jin kamar amarya, baka yi min adalci fa |
| 109. | **ALHAJI:** | Ah safiya, dalilin aure shine samun yaya, nayi tunanin yanzu yakamata kin samu juna biyu |
| 110. | **SAFIYA:** | Ai bani zan ba kaina ciki ba |
| 111. | **ALHAJI:** | **(ANNOYED)** Tor, me kike nufi da hakan? |
| 112. | **SAFIYA:** | Ni dai abin da naki cewa shine ka binciki kanka kafin ka zargi wani, Alhaji. Kasan dai na dau ciki cikin yan watanni farko a auren da nayi na baya. |

| | | |
|---|---|---|
| 113. | **ALHAJI:** | Tor? Ai nima ina da yara mata uku! |
| 114. | **SAFIYA:** | Alhaji, ka dai san an sanka da aure – saki, saboda neman yaya. Ba ka tunanin cewa …. |
| 115. | **ALHAJI:** | **(INTERRUPTS, INCENSED)** Duk wadan chan matan suna da karara ta rashen daukar ciki karam ki ai safiya! |
| 116. | **SAFIYA:** | **Alhaji,** Ina da tabbas akan kaina, zan kuma iya zuwa asibitin mu na alumna don sake duban kaina, |
| 117. | **ALHAJI:** | **(EXCLAIMS)** Ai hanyar tabbatar wa shine kid au ciki ki haifi da' kawai! |
| 118. | **SAFIYA:** | **(CALMLY)** Alhaji ba amfanin musu, muje asibitin mu na al'umar a duba mu kawai |
| 119. | **ALHAJI:** | Ki ce ke bukatar zuwa asibitin ki bincike kanki, ni lafiyata lau |
| 120. | **SAFIYA:** | Abinda z aka fada kenan Alhaji? Ba damuwa zan je mako mai zuwa insha Allah |
| 121. | **ALHAJI:** | safiya sam! Gobe da safe zaki je! |
| 122. | **SAFIYA:** | **(FRUSTRATED)** Tor, Alhaji na ji. Insha Allah gobe zan je asibitin, amma zan sha mamaki abinda za k ace bayan a tabbatar lafiya ta. |
| 123. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |